


A cikin duniya ayau, akwai hanyoyi dabam daban na kariya ta hanyar tsare lafiya, kariya domin marasa galihu, kariya ta rai, da jingina, kariyan dukiya, kariyan bashi da ta mota da sauransu. Wani mai kwarewa a fanin kariya yace idan an zo batun neman shiga kariya, wani abu asakiya zai sa yarjeniya ta rushe. Sakiya tana da hatsari. Abatun kariya, abuduwa uku masu karfi sune rai, nakasarwa da lafiyan jiki. Amma mafi muhimminci shine rai.

Abin mamaki ne yadda mutane na kashe lokaci da dukiya domin kariyan gidaje, motoci da wadansu ababa na rayuwa da suka mallaka amma ba su tabba yin tunani mai zurfi gama da kariyan abu mafi mukimmanci da Allah ya basu (Wato rai). Mutane da dama sun yi kariyan ransu da ma'aikatar kariya (Ishuwara) amma wannan bata zama cikaken tsaro ba domin bata dawama har abada ba. Ko da menene burin mutum a rayuwa, kana bukata hikimma da lokaci domin tunani akan muhimmancin rayuwa da hakikanci cewa wata rana zaka mutu ka koma zuwa ga duniya na har abada kuma duk idan ka iske kan ka bayan mutuwa can zaka dawama har abada abadin. Abin takaicine ace mutum yana sone mutum ya yi tsaron ransa na wushen – gadi. Wauta ne mun bar ran mu a hannun mutum mai mutuwa wanda shi ma bai iya Karin kansa daga mutuwa ba.

Lokacin da ubangiji Yesu yana cikin duniya, ya badda labari na ban ranzana gama da wani mutum mai arziki wanda yana cike da buri tattalin samu mallakar duniya amma bai da shirin komowa gida na har abada. Allah ce da wannan mutum wawa! (Luka 12:16-21). Wawanci shine mutum wanda rayuwar sa da lokacinsa ya na kan tattalin tara abubuwa na wannan duniya mai kare-wa amma ya bar abinda ya kamata- ransa- ba shiri. Yesu yace … Rayuwar mutum bai danganta akan abubuwa da ya tara ba" (Luka 12:15). Ya kuma ce acikin Markus 8:36,37, " Menene riba da mutum zai samu, ya sami dukan duniya ya kuma rasa ransa? Me mutum zai bayar don musayan ransa?

Babban makami da shaidan ke amfani da shi, shine rudu. Idan baka da shiri na komowa a rayuwar har abada, yana nuna kena an rude ka (Watau ibilis ya yauda-re ka). Yesu yace shaidan ya zo domin yayi sata, yayi kisa da kuma hallakaswa (Yahaya 10:10). Amma Yesu ya zo domin ya bamu rai, ba rai na jiki kawai ba amma madawamin rai. Wannan itace rai da Allah yake bayar, kuma ba mutum da zai sami ta sai dai an maya haifuwarsa, ta haka sai ya zama dan Allah. Allah zai zama uba agare shi, shi kuma zai zama dan Allah. Wannan rai da uban yana da shi, shine zai zama daidai da na dan!.

Gagarumin nasara da mutum zai iya yi a rayuwa shine ya gani bukata mai ceto. Watan wata rana ko mu ki ko mu so; Kowane mutum na miji da ta mace zai fuskan ce lahira. Tambayya da ta rage yanzu shine inane zaka kasance har abada abin. Zaka yi rayuwa na

har abada ko tare da Allah, ko acikin wuta tare da Ibilis da dukan abokan gaban Allah. Allah ya ba kowanne mutum lokaci domin yaji bisharan Yesu Almasihu, mai ceton duniya, akala sau daya a rayuwa da kuma yadda ya mayar da martani da bishara da ya ji ya rage ruwansa. Mai yuwa wannan ba shine far-kon jin bisharanka ba akan Yesu Almasihu. Menene zaka yi yanzu da bisshara? Ba wai sai ka dandana wutan jaharnama kafi ka gaskanta a kwai jaharnama ba. Me zai hana ka yanzu ka yi zabe idan zaka kasance har abada da shike kana da wannan zarfi.

Allah yana da matsayi. Allah ba zaya sharanta ka bisa matsayi ka, amma bisa ga matsayinsa wadan ke cikake da ba ko mutum da zaya iya kaiwa. Littafi mai Tsarki ta bayyana mana cewa kowane mutum mai kasawa ne ta wurin zunubi. Kuma ya dace ya fuskanci sharia- kayaswa na har abada (Romawa 3:23; 6:23). Yesu shine maganin Allah domin wannan babbar damuwa. Yesu ya zo ya mutu a wurin mutum, ya dauke zunuban mutum, ya kasawada hukunci. A yau kowane mutum daya bada gasikya gare shi ya karbi Yesu Kristi –kyautar Allah ga mutane –zaya zama da adalchi bisa ga matsayin Allah. Adalchin mutum agaban Allah kazanta ne kawai (Ishaya 64:6). Ayukan mu masu kyau basu da iko su cece mu. Zuwa ekklisiya ba zata cece ka ba kamar kwana a wurin gyaran motoci ba zaya mad da kai mota ba.

Yesu yace: “Gama Allah yayi kaunar duniya har ya badda Dansa makadaici domin dukan mai bada gaskiya agare shi kada ya lalace amma ya sami rai na har abada.” (Yahaya 3:16). Wannan shine begen mu kadai- kaunar Allah an bayyana shi ta wurin Dansa Yesu Almasihu. Idan kana son ka kare ko ka tsare ranka awurin Allah, sai kayi wannan adu'a mai sauki zuwa ga Allah da gaskiya. Allah zai ji ka nan take yayin da kira shi:

*“Ya Allah, na gode maka da ka badda Danka Yesu ya mutu domin zunubana, wanda ya sa na sami rai na har abada a maimakon mutuwa madawami. Na furta Yesu Kristi ya zama ubangiji da mai ceto, na kuma bada gaskiya cikin zuciya-ta cewa ka tashe shi daga mattatu domin in kubuta. Bisa ga maganar ka na furta cewa na sami ceto; ni sabon haifuwa ne, ina da rai na harabada yanzu. Ina roko ka, ka cika ni da Ruhun mai Tsarki ka kuma tai-make ni, in hadu da manufar rayuwarta. Na gode Uba, cikin sunar Yesu. Amin!”*

Na tayya ka murna! Maraba da zuwa cikin iyalin Allah. Yanzu kai sabon haifuwar ne. Yana da kyau ka sami littafi mai Tsarki, ka karanta shi kana kuma addua kowance rana ga Ubanka na sama, kaje ekklisiya da ta gaskanta da littafi mai Tsarki mai koyaswar gaskiya kuma. Za ka iya tuntube mu kuma zamu ji dadi mun taimake da ababa da zasu karfafa bangaskiyar ka cikin Almasihu.

---

Domin ka karbi irin wadan-nan takardu a kyauta domin Bishara da Karin bayani sai ka kira:

**LIFE COMMISSION MINISTRY**
+23470-32138935, +23480-59153304
P. O. Box 8272, Anglo-Jos, Plateau State, Nigeria
www.lifecommission.org / lifecommission@yahoo.com